UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

**FICHE PRATIQUE**

# CUƊANYA DA AL'UMMOMI TA HANYAR WHATSAPP TREES

**WANNAN TAKADDAR SHAIDA TA HAƊU DA AYYUKAN UNHCR DA ABOKAN AIKINTA WAƊANDA SUKA YI AMFANI DA MANHAJOJIN AIKA SAKONNI KAMAR WHATSAPP DOMIN YIN HULƊA DA AL'UMMOMI. YANA BAYANIN YADDA WAƊANNAN MANHAJOJI KE BADA DAMAR YADA BAYANAI WATON "CASCADING" ZUWA KUMA DAGA UNHCR DA ABOKAN AIKIN TA, TA HANYAR KUNGIYOYIN DA AKE KIRA “BISHIYOYIN WHATSAPP”.**

Waɗannan "bishiyoyi" an samo su ta hanyar ƙirar bishiyoyin sadarwa na gargajiya waɗanda aka ƙera su don hanzarta yada bayanai ta wayar tarho, daga mahad'a ta hannun ‘yan al'umma.

"Bishiyoyin WhatsApp" ɗaya ne daga cikin tashoshin sadarwa masu yawa kuma dole ne a haɗa shi da wasu tashoshi don samun ingantaccen dabarun haɗin gwiwar al'umma, a saman yanar gizo da kuma ba tare da yanar gizo.

## WANI MANHAJA ZA’A ZAƁA?

Mai fiye da masu amfani biliyan biyu (2) a fadin duniya, WhatsApp shi ne zaɓi "kai tsaye". Amma, yana da mahimmanci a fara tuntuɓar al'ummomi, saboda WhatsApp na iya zama ba manhajar da suka fi so ba (ko kuma ba ya samuwa a wasu yanayin ayyuka).

### YI:

- Gudanar da kimantawa game da bayanai da sadarwa na yanayin domin samun fahimtar mafificin hanyoyin sadarwar al'ummomi (haɗe da yare) da kuma gano tashoshin da suka fi amincewa da su.
- Yi la'akari da darajar amfani da manhajojin aika saƙonni da dama idan an gane cewa ƙungiyoyin masu amfani na da fifiko daban-daban.

## TSARIN AIKI

Manufar "WhatsApp tree" shine yada bayanai daga ko kuma zuwa wani cibiya zuwa wasu shafufuka da dama da masu karɓa.

UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FICHE PRATIQUE

**Bishiyar WhatsApp mai yaduwa**




## MEMBOBI NAWA NE A KOWANE GUNGU?

Gungun WhatsApp na iya ƙunsar membobi 256. Darussan da aka koya daga UNHCR ya nuna cewa tabbas wannan ba shine daidaitaccen lamba na gungu a cikin ƙirar "bishiyoyin WhatsApp" ba.

Kirƙirar gungu mai dauke da mahalarta 10 yana taimakawa wajen gudanar da kwararar bayanai a bangarorin shiga da fita. Wannan yana ba wuraren bayanai damar gani da kuma amsa saƙonni a kan kari, ba tare da ya zama aiki na ko wane lokaci ba.

Yana da sauƙin tafiyad da mutane 256 a cikin gungu da aka shirya a matsayin "jerin aikawasiku". Jerin aikawasiku ya kunshi jerin da ka adana masu ƙarba wanda za'a iya aikawa saƙon iri ɗaya akai-akai ba tare da an zaɓe su a kowane lokaci.

## KIRKIRO DA RABA BAYANAI

Bishiyoyin WhatsApp na baiwa UNHCR da abokan aikin ta damar raba bayanai ta hanyar rubutu, hotuna, sauti da bidiyo. Abun ciki wanda ke da ƙaranci ko rashin rubutu na iya zama mafi fifiko ga gungun masu ƙarancin ilimi da abun ciki mai ɗauke da sauti/bidiyo na iya zama mafi sauƙi ga mutanen da ke da nakasa. Bayanai da sadarwa na buƙatar ƙididdiga wanda zai taimaka wajen gano nau'in abubuwan da gungun daban-daban suka fi so a cikin al'umma.

Kafin a yada sauti, bidiyo da abun ciki na hoto, yana da mahimmanci a san ko akwai wata cikas na samun damar irin waɗanan abubuwan ciki. Wata ƙila mutane ba sa so ko za su iya samun dama ga wasu abun ciki na sauti da hoton bidiyo saboda amfani da data da farashi.

FICHE PRATIQUE

**Yi:**

- Gwada nau'i daban-daban na abun cikin sauti da hoton bidiyo tare da wasu gungun daban-daban.
- Duba makin shuɗi don ganin ko an kunna abun ko an saurari abun ciki.
- Tambayi masu amfani don samun tsokaci a kan abun cikin. Ta yaya za a iya daidaita shi ko inganta shi?

## SAMAR DA AMINCI

Lokacin yada abun ciki, yana da mahimmanci a nuna daga in da ya zo (misali daga Ofishin UNHCR's Na Gida X). Hakanan yana da mahimmanci a tabbatar da cewa bayanin da aka yada ba'a saman yanar gizo ya zamanto iri guda.

**Yi:**

- Kafa hanyoyin haɓakawa da raba bayanai da kuma tabbatar da cewa kowane cibiya da mai karɓa ya fahimta.
- Yi cuɗanya da tsare-tsaren daidaituwa na gida da suka dace (misali Communication and Community Engagement (CCE) Working Group in suna aiki) don tabbatar da cewa bayanan da aka raba daidai ne.
- A rage yada bayanan ƙarya da kuma tabbatar da cewa wuraren da aka mai da hankali suna sane da nauyin da ke kansu.

## RA'AYI DA SHAWARA

Kamar yadda membobin alumma ke raba bayanai ta hanyar "bishiyoyin WhatsApp", yana da matukar mahimmanci UNHCR da abokan aikinta suna mai da martani ga wannan bayanin.

Kamar yadda ake da sauran kayan aiki na karɓar ra'ayoyi, ana buƙatar tsarin turawa gaba - ba tare da wannan ba, membobin al'umma za su rasa amincewa da hanyar da sauri. Ya kamata a ƙafa tsayayyen hanyoyin aiki kuma a sa ido saboda ma'aikata na musamman zasu san yaushe, zuwa waaye kuma ta yaya zasu tura tambayoyi masu zuwa, tsokaci da korafe-korafe.

FICHE PRATIQUE

**Yi:**

- Kafa tsayayyen hanyoyin aiki don ra'ayoyin jama'a da korafe-korafe tun daga fari kuma tabbatar cewa an turawa abokanai aiki, ma'aikata na musamman da masu amfani dashi daga ƙarshe kuma su fahimce shi.

- Tabbatar cewa bishiyar WhatsApp ɗin an haɗa shi a cikin tsarurrukan karɓar ra'ayoyi da maida amsa gabadaya.

- Yi amfani da wasu hanyoyin maida amsa (misali fuska da fuska) idan ha dace - musamman don korafe-korafen sirri.

## KARE BAYANAI

Duk da dai WhatsApp suna bada tsarin kariya na end-to-end encryption don tabbatar da sirrin sakonni, ba'a bada shawarar wallafa bayanai kai da zai sa a gano mutum saboda akwai ƙarin haɗarin wani daga waje zai samu damar shi, a ƙara wallafa kuma a yi amfani dashi ta hanyar da bai dace ba. Saboda haka ya kamata a tura mutane zuwa wasu hanyoyi masu tsaro don bada wannan bayanin.
A "bishiyoyin WhatsApp", gungun daban-daban zasu yi dangantaka da ƙungiyoyi daban-daban da mambobin al'umma daban-daban. Yayin da dole ne a bada bayanai sirri ta WhatsApp, ya kamata sakamakon wannan bada bayanin ya bambanta bisa ga mutanen da abun ya shafa da kuma ƙungiyar da sukewa aiki. Bada bayani a cikin ƙungiya ɗaya yafi sauki; tare da wani abokin aiki wanda ke bin ka'idar UNHCR na tsare bayanai akan ɗai-ɗaikun mutanen da ake nufa (wannan yawanci haka ne tare da haɗin gwiwa da UNHCR).

**Yi:**

- Yi la'akari da menene ya ƙunsa tura bayanai tsakanin ƙungiyoyi da kuma da wasu ɗai-ɗaikun mutane idan suna cikin wani bishiyar WhatsApp
- Shirya wasu hanyoyin tura bayanai sirri, duk a ciki da tsakanin ƙungiyoyi, kuma koma kansu idan ya zama dole.

## SIRRIN BAYANAI

Babban abun dake jawo matsalolin sirri shine cewa masu amfani basa sabe akan sakamakon tura bayanai. Ya kamata masu amfani suna sane cewa lokacin da suka shiga gungun akan WhatsApp, duk masu amfani a cikin gungun na iya samun lambar wayar su. Hakan kuma, su ma zasu samu damar lambobin sauran masu amfani. Dole su bada izinin wannan kuma su yi abun da ya dace.

Ya kamata akwai hanyoyin rage da hukunci (kamar fitar dasu daga bishiyar WhatsApp ɗin) don masu amfani da basa amfani dashi yadda ya dace.

UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

## FICHE PRATIQUE

Masu gudanar da wani gungun na WhatsApp na iya tura gungun ta wani mahada. Yayin da hakan zai bari a wallafa gungun sosai a cikin al'umma, zai iya bada dama wasu mutanen da ba'a amince dasu su samu damar gungun WhatsApp ɗin, saboda waɗannan mahadar basu da “sirri".

### Yi:

- Bada shawara da jagora ga masu halartar akan abubuwan da za'a yi da wanda ba za'ayi ba game da wallafa bayanai a cikin gungun WhatsApp a matsayin wani ɓangaren bishiyar.
- Tabbatar cewa ma'aikata na musamman da masu amfani a ƙarshe sun fahimci saitunan sirrance bayanai na nasu shafukan. Zaka iya wallafa bayani game da wannan a lokacin ƙirƙiro sabin gungun da kuma a lokacin tura sakonni na yau da kullum.
- Rage tura gungun ta mahada sosai don gujin wanda ba'a amince dasu su samu dama da kuma shaidar mahadar akan shafukan bincike.

## MISALAI DOKOKIN MU'AMALA DON WANI GUNGUN

- Koyaushe a girmamawa dalilin ƙirƙiro gungun! Kada a tura sakonni game da wasu batutuwa.
- Kada a yada bayanai da ba'a tabbatar ba. Sai bayanai da UN da UNHCR suka tabbatar za'a amince dashi.
- Kada a yi banza da gungun! Bayani mai yawa yana kashe bayanin; kuma yi tunani game da lokacin da kake tura sakonnin ka.
- Idan wani yayi tambaya kuma baka san amsar ba, kada ka amsa da “Ban sani ba". Kawai jira wani wanda yasan amsar.
- Kada kuyi hira da juna a cikin gungun. Yi amfani da naku shafin don wancan.
- Kada ku tura sakonnin “nagode" sau dari. Idan kana godewa wani, faɗa mishi ta shafin shi.
- Kada ku tura wani bayanin sirri game da gungun.
- Tuna cewa abubuwan da UN suka darajanta da dokokin aiki sun shafi wannan gungun.



Plus d'outils
et de conseils
pour communiquer avec les communautés sur le site :
cwc.westafrica.exposed